# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Ikkilisya ta sadu da Damuwa

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Kwanaki hamsin bayan da Yesu Dan Allah ya tashi daga matattu, Ruhu Mai Tsarki ya sauko domin ya kasance tare da masu binsa.  Ko da yake almajiran ba su gane yadda Allah Uba, Allah Da (Yesu) da Allah Ruhu Mai Tsarki zai iya zama daya ba, su dai suna da farin ciki cewa Allah yana tare da su.  Allah ya yi abubuwa masu ban mamaki domin ya taimake manzanin su fada wa wadansu game da Yesu.**



**Mutanen da sun ba da gaskiya ga Yesu sun raba duk abin da suke da shi tare domin talakawa su ma su samu. Amma akwai wani iyali mai suna Ananiyas da Safira wanda sun kasance da rashin gaskiya. Sun sayar da wani gona sai suka yi kamar sun kawo duka kudin wa manzanin. A boye, sai suka ajiye wadansu kudin wa kansu.**



“Don me Shaidan ya cika zuciyarka domin ka yi karya wa Ruhu Mai Tsarki…?”

Bitrus ya tambaye Ananiyas. “Ba mutane ba ne ka yi musu karya, amma Allah ne.” Nan Annaniyas ya fadi kasa ya yi numfashinsa na karshe. Sai matasa suka rufe shi suka dauke shi zuwa waje suka binne shi.



**Dan lokaci kadan an jima, Safira ta shiga, ba ta san cewa maigidanta ya mutu ba.  Sai ita ma ta yi karya game da kudin – ita ma abin da ya faru da maigidanta haka ya faru da ita.  Babban tsoro ya kama duk wadanda suka ji abubuwan nan.**



**Allah Ruhu Mai Tsarki ya yi al’amura da al’ajibai ta hannun Manzanin. Misali, an warkar da marar lafiya sa’ad da inuwan Bitrus ya fadi a kansu.**



**Lokaci ne na manyan ayyukan al'ajibi, masu nuna kasancewar Allah. Mutane yau da kullum suna ba da gaskiya ga Yesu. Wannan ya sa Babban Firist ya yi fushi.**

**Ya sa aka rufe manazanin a kurkuku.**





**Amma da daddare mala’ika daga Ubangiji ya bude kofofin kurkukun ya fitar da su, ya ce, “Tafi, tsaya a cikin haikalin ka yi magana da mutanen game da kalmomin rai.” Manzanin suka fita waje suka fara wa’azi game da Yesu. Da safe, mazan Babban Firist suka same kurkukun ba kowa a ciki.**

**Sa’ad da ya same shi a karshe, Babban Firist ya yi wa manzanin fada. “Ba mu gaya muku kada ku yi koyarwa a wannan Suna ba?” “Yakamata mu yi biyayya ga Allah maimako mutane,” Bitrus da sauran almajiran suka amsa. Babban Firist ya yi fushi sosai, sai ya so ya kashe manzanin. Maimako, sai ya umarta a dudduke su sai a bar su su tafi. Duk da zafin da suke a ciki, manazanin sun yi biyayya ga Allah suka ci gaba da wa’azi game da Yesu.**



**Wata rana aka kama wani mutum mai suna Istifanus. Istifanus yana kaunar Ubangiji Yesu. Ruhu Mai Tsarki yana amfani da shi don ya fada wa wadansu labarin Yesu. Wadansu maza suka yi karya, suna cewaIstifanus yana maganar zagi ga Allah. Bayan da suka bincike shi a hanyar da ba daidaiba, sai aka jejjefe shi da duwatsu har mutuwa.**



Kafin ya mutu, Istifanus, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya daga idanu sama sai ya ga daukakar Allah Yesu kuma yana tsaye a hannun daman Allah.  Taron jama’a suna ta jejjefe shi yayinda yana kira ga Allah yana cewa, “Ubangiji Yesu, karbi raina.”



**Sa’an nan, kamar Yesu a kan giciye, wannan mutum mai karfin hali ya yi amfani da numfanshinsa na karshe ya yi addu’a domin Allah ya yafe wa wadanda suka yi masa kisa.**



**Mutuwar Istifanus ya ta da wani sabowar tsanantawa. Wani saurayi mai suna Shawulu, wanda ya taimake masu kisan Istifanus, ya kakkama kowane Kiristan da ya gani. Yawancinsu suka gudu daga gidajensu suka bazzu ko’ina a Yahudiya da Samariya. Manzanin ne kadai suka zauna a Urushalima.**



**Ko da yake abokan gabansu sun so su kashe su, wadanda suka bazzu suka tafi ko’ina suna wa’azi labari mai dadi game da Yesu.  Babu wani abu wanda zai iya tsai da masu bin Yesu – saboda Ruhu Mai Tsarki na Allah yana a cikinsu kuma yana aiki ta wurinsu.**



# Ikkilisya ta sadu da Damuwa

# Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

# a na samu a

# Ayyukan Manzani 5-7

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

56

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin
Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da
Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**